# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kowa dabam Allah ya yi shi: Mutunta haƙƙin tsirarru
## Kashi na farko: Shaharren zabiya ɗan ƙasar Zambiya


Wanda ya rubuta: Adrian Kriesch
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling


**'Yan Wasa:**

Mai ba da labari

| | |
|---|---|
| John Chiti: | ɗan shekara 27 |
| Herbert Kirchesch: | ɗan shekara 50 |
| Jonathan Muswi: | ɗan shekara 34 |
| Lista Motokwa: | 'yar shekara 25 |

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin kashi na farko cikin wani sabon shirinmu na “Ji Ka Karu” mai suna “Kowa Dabam Allah Ya Yi Shi - Mutunta Haƙƙin Tsirarru”. A cikin wannan shirin za mu gana ne da ƙungiyoyi dabam-dabam, musamman na marasa rinjaye a Afirka. Su mutane ne kamar kowa, amma ta yiwu kamannin waɗansunsu sun ɗan bambanta da na sauran mutane, haka ma tunaninsu, ko ma ta yiwu suna da wasu aƙidu game da rayuwa da suka bambanta da na mafiya rinjaye daga mutane, wanda duk waɗannan bambance-bambance na iya jawowa a ƙyamace su. Amma duk da hakan sukan ci gaba da neman haƙƙoƙinsu.

To a yau za mu duba al’amarin mutanen da ake kira zabiya ne wanda wani yanayi ne da yake faruwa saboda ƙaranci ko rashin wani sinadari na halitta a fatar jikin mutum, wanda kan sa fatar mutum ta zama fara fat. Wannan yanayin yana sa wa su zama dabam, musamman ma a Afirka. A wani lokacin ma akan kai musu farmaki ko ma a kashe su, saboda rashin fahimtar yadda suka samu kansu a wannan yanayi. A yau za mu gana ne da wani matashi da aka dinga ƙyamata tun yana yaro saboda kamanninsa sun bambanta da na sauran mutane. Amma a halin yanzu ya shahara sosai a ƙasarsu.

**Bayanin John Chiti cikin Turanci:**

*“Sunana John Chiti. Ni zabiya ne, ina kuma zaune ne a Lusaka a ƙasar Zambiya. Ni mawaƙi ne kuma ni ne na kafa Kungiyar Zabiya ta ƙasar Zambiya, sannan ni ne shugabanta.”*

**Mai ba da labari:**

John Chiti mutum ne mai matuƙar sha’awar kiɗa da waƙa. Za ka iya fahimtar hakan ƙarara idan ka ga yadda yakan miƙe tsaye idanunsa a rufe riƙe da lasifika a wata ƙaramar ‘studio’ ɗinsa. Kwanan nan ya fitar da wata sabuwar waƙar soyayya mai suna “Komai Zan-zan a Zambiya”. Wannan waƙa ce ta fito da shi a shekarar 2008. A lokacin John bai daɗe da baro ƙauyensu zuwa babban birnin ƙasar ba. Zuwansa ke nan sai wani mai shirya waƙoƙi ya gano basirar da yake da ita ta waƙa, sai kuwa ga shi waƙar da ya yi ta farko ta

zama sanadin fitowarsa. Tun daga wannan lokacin kalar jikin John sai ta zama gobarar titi a gare shi.

**Bayanin John Chiti cikin Turanci**

*"Akwai mutanen da idan suka zo kallon wasana, kai tsaye suke zarcewa wurin da nake yin waƙa. Irin waɗannan mutanen sai ka ji sun ce, "ashe dai shi ɗin ne kuwa yake waƙar!". Da sun ɗauka akwai wanda yake waƙar a ɓoye a wani wuri, ni kwaikwaya kawai nake yi. Ni kuma sai na zuba musu ido kawai! Sai su ma ka ga sun ƙura min ido suna kallon kalar jikina, sai ka ji sun ce, "abin mamaki!".*

**Mai ba da labari:**

Yayin da John yake ƙarami har ya fara tasowa ba kasafai yake jin an yabe shi ba, ko kuma a dinga faɗa masa maganganu masu ƙarfafa gwiwa. Babansa ya guje su lokacin da aka haife shi saboda bai yarda cewa ɗan da ya haifa zai iya fitowa haka fari fat ba. A tunaninsa babar John a waje ta samo cikinsa wanda idan ba haka ba, to ta yaya John bai zo baƙi ba kamar yadda sauran 'yan'uwansa suke baƙaƙe! Bai san cewa iyayen da ba zabiya ba na iya haifar zabiya. Duk da cewa ana samun kalar fatar jikin iyaye ta zama irin ta kowa, ta iya yiwuwa kuma suna ɗauke da wata ƙwayar gadon halitta a jikin nasu da za ta iya jawowa wani daga cikin 'ya'yan da suka haifa ya zama zabiya, kamar dai yadda wani likita ɗan ƙasar Jamus, wato Dr. Herbert Kirchesch, ya yi bayani.

**Bayanin Dr. Herbert Kirchesch cikin Jamusanci:**

*"Hakan kan faru yayin da aka samu cikin mutum. Kwayoyin gadon halittar da ake gada daga iyaye ana harhaɗa su ne ba tare ba bin wani tsari ba, kamar dai yadda ake gara ɗan ludo. Wannan shi ne dalilin da ya sa kowane mutum yake dabam. Ana samun bambanci ko yaya yake tsakanin mutane. A cikin ƙwayoyin halittar zabiya akwai sinadarin da babu shi. Ko dai babu wannan ƙwayar halittar a fatarsa, ko gashinsa, ko kuma idonsa kwata-kwata ko kuma ya yi ƙarancin da ba shi da wani tasiri."*

**Mai ba da labari:**

Babbar matsalar da zabiya kan samu ta ɓangaren lafiya guda biyu ce. Saboda rashin wannan sinadarin a jikin fatarsu ba wuya zafin rana ya ƙona ta. Zabiya da dama na rasa ransu a Afirka a dalilin ciwon sankara saboda ba sa samun mayuka ko magungunan da za su ba su kariya daga zafin rana. Haka kuma zabiya ba su da kaifin gani, don kuwa da ƙyar suke iya ganin abu daga nesa. Haka za ka ga suna ƙiƙƙifta idanu don su hango wani abu. Don haka, yana da amfani sosai su dinga zama a gaba a aji.

Bayan wannan matsala da ta shafi lafiyarsu, a mafi yawan ƙasashen Afirka zabiya na fuskantar wariya. Akwai camfe-camfe da yawa akan al'amarinsu. Akan ce zabiya ba sa mutuwa, akan kuma ce ana amfani da gashinsu a haɗa magani. Shi dai John Chiti ba abin da yake yi idan aka yi irin waɗannan maganganu na ƙarya ban da girgiza kai. Kuma duk wannan jita-jitar da ake yaɗawa game da zabiya ba ta taɓa tabbata ba. Yara zabiya kan samu kansu a cikin yanayi mara daɗi saboda nuna musu bambanci da ake yi. Wannan shi ne bayanin da John ya yi yayin da ya tuna ƙuruciyarsa.

**Bayanin John Chiti cikin Turanci:**

*"Sai na fara jina dabam, ba kamar sauran mutane ba. Yayin da na fara wannan tunanin, sai na fara yi wa kaina wasu tambayoyi. Me ya sa haka ne? Me ya sa na bambanta da sauran mutane? Me ya sa mutane suke yi mini dariya? Me ya sa mutane suke tsarta wa inuwarsu yawu idan suka gan ni? Waɗannan tambayoyin duk sai su sa jikinka ya yi sanyi. Sai mutum ya fara tunanin: Ni ba mutum ne kamar kowa ba fa, ba a ƙaunata, ni ba mutumin kirki ba ne. Sai nake ta raina kaina. Ko da zan iya yin wani abu, sai kawai na ƙaskantar da kaina na ce: Ni fa zabiya ne, ba zan iya wannan abu ba."*

**Mai ba da labari:**

Amma duk da waɗannan matsalolin John bai taɓa bayar da kai bori ya hau ba ko kusa. Maimakon haka sai abin ya zama kamar ƙaimi a gare shi. A shekara ta 2008 sai ya kafa Kungiyar Zabiya ta ƙasar Zambiya. Wannan ƙungiya tana ƙoƙarin inganta rayuwar zabiya a ƙasar Zambiya. A halin yanzu 'ya'yanta sun kai kimanin mutum 500. Akasarinsu na zaune ne a babban birnin ƙasar,

amma John yana ta shirye-shiryen buɗe ƙarin ofisoshi a wasu birane na ƙasar don ya gudanar da harkokin ilimantarwa a can ma.

'Yan ƙungiyar na gudanar da taro a kai-a kai, suna kuma tattaunawa a kan abin da ya shafe su. Ta wannan hanyar suke yaƙar wariyar da ake nuna musu. Yawan rahotannin kisan da ake yi wa zabiya yana nuna muhimmancin yin irin wannan taron. A ƙasar Tanzaniya kaɗai, tsakanin shekara ta 2007 zuwa shekara ta 2011, an kashe zabiya da yawansu ya wuce 60, musamman don a sayar da sassan jikinsu ga matsafa. Ana tabka irin wannan munanan laifukan ma a ƙasar Zambiya.

Mun shiga mota zuwa Kanyama, wata unguwa awon igiya da ke cikin Lusaka, inda muka gana da Jonathan Muswi. Mun samu wannan mutum ɗan shekara 34 zaune a kan kujerar roba a ƙofar gidan da yake zaune da iyalinsa har zuwa shekara ta 2011, shekarar da aka kashe 'yarsa mai shekara biyar mai suna Prudence.

**Bayanin Jonathan Muswi cikin Nyanja:**

*"Tafiyar babarta ke nan kasuwa, ita kuma Prudence tana wasa tare da ƙawayenta. Ita yarinya ce mai shiru-shiru. Duk sanda suka yi wata magana da ƙawayenta, sai ta ja jikinta daga cikinsu. Lokacin da babar tata ta dawo daga sayayya ba ta nan. Bayan awa ɗaya sai aka ga gawarta a cikin jaka kusa da makaranta."*

**Mai ba da labari:**

'Yansanda ba su gano dalili ko wani wanda ya aikata laifin ba, amma shi Jonathan ya tabbatar an kashe ta ne don ita zabiya ce. Yana jin wanda ya kashe ta ya yi niyyar tafiya da ita ne don ya sayar, amma ya gudu ya bar gawar tata. Jonathan ya rungume 'yar tasa a hannunsa. Daga ran nan, rayuwarsa ta dagule kamar yadda ya yi bayani. Ya kasa fitar da tunanin Prudence daga ransa. Shi ma kansa sai da ya ji dabam lokacin da aka haifi Prudence. Ita kaɗai ce zabiya a gidan nasa, ya kuma kasa fahimtar haƙiƙanin abin da ya sa haka. Da shi da matarsa da kuma 'ya'yansa guda huɗu duk baƙaƙe ne. Daga nan sai ya nufi wajen Kungiyar Zabiya don neman shawara, ya kuma karɓo man da zai dinga shafa mata a jiki. A nan ya samu bayanin

cewa Prudence mutum ce kamar kowa.

**Bayanin Jonathan cikin Nyanja:**

*"Zabiya mutane ne na ƙwarai. Shekarunta biyar kacal, amma na fahimci cewa 'yata yarinya ce ta gari. Hankalina yakan yi matuƙar tashi idan na ji irin maganganun nan na shirme da mutane suke yi game da zabiya. Duk lokacin da na ji irin waɗannan maganganu, sai duk hankalina ya dugunzuma."*

**Mai ba da labari:**

Yanzu dai misalin ƙarfe bakwai da minti biyar ne na daren ranar Lahadi, a daƙin watsa shirye-shiryen talabijin na TV2. John Chiti ya sake makara. An riga an fara gabatar da wannan shirin da kimanin minti talatin kafin wanda aka gayyata don yin shirin ya shigo. John ya ɗan tattauna da mai shirya shirin a gurguje, sannan aka kuma ci gaba da hira da shi kai tsaye.
Bayan an kammala ganawar ɗaya daga cikin masu gabatar da shirin, wato Lista Motokwa, ta faɗa mana irin tasirin da John ya yi a kan mutanen ƙasar Zambiya.

**Bayanin Lista Motokwa cikin Turanci:**

*"Saboda fitowa fili da John ya yi, ya yi cikakken bayani a kan al'amarin zabiya, mutane irina mun sauya tunaninmu game da su. Na ɗauki zabiya daidai da kowa. Mutum yana tasowa ne da wannan aƙida tun daga yarinta. A Afirka, ana cewa zabiya ba sa mutuwa da dai sauran irin waɗannan camfe-camfen. Amma yanzu wannan tunanin ya fara sauyawa a hankali saboda ana ta wayar da kan mutane game da al'amarin zabiya, yanzu ana sakin jiki da su."*

**Mai ba da labari:**

Shi dai John yana tsaye kusa da Lista yana gyaɗa kai, wato yana nuna amincewa da abin da take faɗa, yana kuma fatan sauran jama'a ma za su fahimci hakan.

**Mai gabatarwa:**

Da wannan muka kawo ƙarshen shirin na yau a kan zabiya wanda Adrian Kriesch ya rubuta mana. Idan kuna son sake sauraron shirye-shiryenmu a kan mutunta haƙƙin tsirarru, sai ku leƙa adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kazalika kuna iya tura mana mana ra'ayoyinku a shafinmu na 'Facebook'. Ku huta lafiya!